JUMHURIYYAR MISRA TA LARABAWA 10 Rajab, 1443
MA'AIKATAR ADDININ MUSULUNCI 11 Febrairu, 2022

(1)

## HATSARIN SAKI

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **(Sulhu alhairi ne..)** [an- Nisa'i: 128], Ina shaida cewa lallai babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina kuma shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammad bawan Allah ne kuma Manzonsa, Ya Allah Ubangiji ka ƙara masa tsira da aminci da albarka, shi da alayensa da sahabbansa, da duk wanda ya bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, Bayan haka:

Lallai addinin Musulunci ya bai wa rayuwar aure wani tsarki na musamman, da matsayi mai girma, ya shimfiɗa mata haƙƙoƙi, da wajibai, da ladubba da za su kiyaye kwanciyar hankali, da natsuwa, da haɗin kai, da kuma cigabanta a cikin wani yanayi na soyayya, da ƙauna, da tausayi, da mutunta juna tsakanin ma'aurata biyu, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Ku rayu da su –matayenku na aure- cikin kyautatawa)** [an- Nisa'i: 19], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Mafi alhairi a cikinku shi ne wanda ya fi zama alhairi ga iyalansa).**

Wanda duk yake yi Alƙur'ani mai girma kallo na lura zai ga inda Allah mai girma da buwaya ya kira aure da sunan **"yarjejeniya mai ƙarfin gaske"**; saboda ya nuna cewa wajibi ne a girmama shi, kana kuma ya yi gargaɗi game da duk wani yunƙuri na rusa shi, ko warware shi, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Mata sun amshi yarjejeniya mai ƙarfin gaske daga gare ku)** [an- Nisa'i: 21]

Lallai Shari'ar Musulunci ta yi kira zuwa ga ma'aurata akan kowannensu ya kalli abokin rayuwarsa da idanuwan adalci, ya kuma yi tunani akan ɓangaren alhairan abokin zamansa, a kullum ya riƙa tuno sifofin alhairi; saboda a samu dawwamar rayuwar aure, da kwanciyar hankali, da samun natsuwa, da ma kyautata gudanar da rayuwa, da jin daɗin zuriya, da iyali, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Ku rayu da su –mata- cikin yanayi na kyautatawa, idan ma kun ƙi su, to ku sani sau da yawa za ku ƙi wani abu, Allah Maɗaukakin Sarki kuma ya sanya alhairi mai yawa a cikinsa)** [an-Nisa'i: 19], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Kada wani mumini ya ƙi mumina –yana nufin matarsa- domin in ya ƙi wata ɗabi'a a tare da ita, zai so wata ɗabi'ar)**, kamala ta Allah ce shi kaɗai, mutum tara yake bai cika goma ba, Annabawa ne kawai suke da Isma, alhairin Allah ya kai zuwa ga wanda yake cewa: **"Wane ne ɗabi'unsa gaba ɗaya suke yardar da kowa? Ai ya isa mutum girma a ce ana iya ƙididdige aibobinsa".**

Lallai babu shakka akan sami saɓani tsakanin ma'aurata a wasu lokuta, wani abu yakan iya giftawa ya dagula tsaftar rayuwar jin daɗi tsakanin mata da miji; saboda haka ne Alƙur'ani mai girma ya samar da cikakken maganin da zai magance irin wannan yanayi, Musulunci ya bayyana cewa alhairi a koda yaushe yana ciki sulhu, da ƙoƙarin yardar da juna, da kuma kyautata wa juna, Allah mai girma yana cewa: **(Idan matar aure ta ji tsoron kada mijinta ya yi watsi da al'amurran gida, ko ya juya mata baya, to, babu laifi idan suka yi sulhu a tsakaninsu, sulhun da zai yi sanadiyyar kusanto da su zuwa ga juna. Mai hankalin cikinsu shi ne yake fara bijiro da batun sulhu, shi sulhu a kowane lokaci alhairi ne, babu sharri a cikinsa, lallai**

**abin da yake hana yin sulhu shi ne kowa daga cikin miji da matan ya dage akan matsayin da yake a kai na sai ya sami duka haƙƙoƙinsa; saboda ƙwauro ya riga ya mamaye zuciyarsa, babu wata hanya ta dawwamar soyayya tsakanin ɓangarorin biyu sai ta hanyar yafiya da rangwamen da ɗaya daga cikin ɓangarorin zai yi, wannan ɓangare mai yafiya da rangwame shi ne mai kyautatawa da tsoron Allah, duk wanda ya aikata aiki mai kyau, ya kuma ji tsoron Allah, to, kuwa lallai Allah yana sane da aikinsa, zai kuma saka masa akan haka)** [an- Nisa'i: 128], idan kuma al'amarin ya buƙaci sai masu hankali, da hikima, da ƙwararru, da mutanen kirki, masu tsoron Allah cikin iyalai da dangogin ma'auratan sun shiga tsakani, to kuwa lallai su shiga tsakanin ne da niyya kawo gyara, da kawar da saɓani, Allah mai girma yana cewa: **(Idan aka sami saɓani a tsakanin ma'aurata biyu, kuka kuma ji tsoron kada ya girma ya kai ga rikicin da zai kai su ga rabuwa, to, ku zaɓi masu sulhu guda biyu: ɗaya daga danginsa, ɗayan kuma daga danginta. In dai sun yi nufin kawo gyara, to, lallai Allah zai datar da su zuwa ga abin da yake shi ne alhairi ga ma'auratan, ko dai su cigaba da zaman auren cikin kyautata wa juna, ko kuma su rabu cikin mutunci. Lallai Allah yana riskar duk wani abu na zahiri da baɗinin da yake tattare da bayi)** [an- Nisa'i: 35], lallai akwai lada mai yawa da Allah zai bayar akan haka, Allah mabuwayi yana cewa: **(A mafi yawan lokuta babu wani alhairi tattare da mutanen da suke ɓoye maganganun da suke yi a cikin zukatansu, ko waɗanda suke yi tsakaninsu da juna; saboda sharri ne ake ɓoye shi, sai dai idan abin da aka ɓoyen ya zamo bayar da umurni ne da yin sadaka, ko aikata wani aiki mai kyau, ko daidaita tsakanin mutane da gyara zumunta, waɗannan kam duka alhairai ne, duk wanda ya**

**aikata haka saboda neman yardar Allah Maɗaukakin Sarki, to kuwa lallai Allah Maɗaukakin Sarki zai ba shi babban sakamako a nan duniya da lahira; saboda abin da ya aikata)** [an-Nisa'i: 114], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Shin ba na ba ku labarin abin da ya fi daraja sama da sallah, da azumi, da sadaka ba? sai suka ce: a faɗa mana, sai ya ce: gyara dangantaka tsakanin mutane biyu da suke da saɓani da juna).**

Amma idan al'amarin ya kai matakin da ake ganin cewa babu yanda za a yi rayuwar aure ta tafi a haka, to a nan addinin Musulunci ya shiryatar zuwa ga yin jinkiri, da natsuwa na wani lokaci, har sai al'amurra sun lafa, zukata sun yi sanyi, inda hankali ya dawo jiki, a lokacin sai a yi bita, a kuma yi duk abin da za a iya wajen dawo da daidaito, za a yi haka ne da niyyar cigaban zaman iyalai ba tare da rabuwa ba.

***

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga fiyayyen halitta, shugabanmu Annabi Muhammadu da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

Lallai babu shakka cewa saki rusa gidan da Allah ya bayar da umurnin a gina shi akan natsuwa, da kwanciyar hankali, da soyayya, da tausayi ne, haka ma saki yana ɗauke da munanan hatsarurruka a rayuwar iyali, da zamantakewa, musamman akan 'ya'ya, idan mun lura da irin yanda suke tasirantuwa mai muni idan iyayensu suka rabu, inda suke fuskantar matsaloli na hankali, da na zamantakewa, da na tattalin arziki, sukan rasa ginshiƙan tarbiyya mai kyau, da tashi akan turba mai kyau, ganin cewa gidansu da yake ɗauke da uwa da uba ya tarwatse, abin da

hakan yake haifar da tashin hankali a cikin zukatansu, yakan kuma zama sanadin na jinkirin karatu, waɗanda duka wannan sharan fage ne na aukawa cikin munanan ɗabi'u, kuma irin waɗannan 'ya'ya ne ƙungiyoyin 'yan ta'adda, da masu tashin hankali, da masu tsattsauran ra'ayi suke farauta, saboda haka ne shaiɗan yake yi iya duk abin da zai iya wajen karkatar da ma'aurata biyu zuwa ga saɓanin da zai kai su ga rusa gidan aure, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Lallai shaiɗan yakan ɗaura kujerarsa akan ruwa, sannan ya tura rundunar yaransa, wanda ya fi kusa da shi a cikinsu shi ne wanda ya fi haddasa fitina, wani daga cikinsu yakan zo ya ce: ai na yi kaza da kaza, sai ya ce masa: ai ba ka yi komai ba, sai wani ya zo ya ce: ai ban bar su ba sai da na raba shi da matarsa, sai ya kusanto da shi, ya ce: kai madalla da wannan abu da ka yi)**, wannan zai wajabta mana mu yi aiki da hankali, kuma a farke saboda mu hana wa shaiɗan duk hanyoyin da yake bi domin ƙulla makirce- makircensa.

Lallai akwai matuƙar buƙatar a sami daidaito, da mutunta juna, da soyayya a tsakanin mutanen da suke rayuwa a gidan aure, wanda haka ne zai kai zuwa ga samun haɗin kai, da kwanciyar hankali tsakanin dukan al'umma baki ɗaya.

**Ya Allah Ubangiji ka daidaita zukatanmu, ka kuma gyara tsakaninmu.**